Ya kai yaro, ka ambaci Allah, ka ci da damanka, ka ci abin da ke gabanka

Daga Umar ɗan Abu Salama - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Na kasance yaro a kulawar Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -, hannuna ya kasance yana yawo a faranti, sai Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce da ni: "Ya kai yaro, ka ambaci Allah, ka ci da damanka, ka ci abin da ke gabanka" hakan bai gushe ba shi ne irin cin abincina bayan nan.

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Umar Dan Abu Salama - Allah Ya yarda da su - ɗan matar Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - Ummu salamah - Allah Ya yarda da ita - yana ba da labari - (cewa) ya kasance ƙarƙashin renonsa da kulawarsa -, cewa ya kasance a tsakiyar cin abinci yana yawo da hannunsa asasannin ƙwarya (kwanon abin ci) don ya ɗauki abincin, sai Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya sanar da shi ladubba uku daga ladubban cin abinci. Na farkonsu: Faɗin "Da sunan Allah" a farkon ci. Na biyunsu: Cin abinci da dama. Na ukunsu: Cin abinci daga ɓangaren da yake kusa daga gare shi na abincin.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/58120